


# Cikakkiyar Musanya

*Yesu ya mutu da mutuwarmu domin mu sami ran Sa*



Furta Kalmar Allah
Daga Derek Prince

> "Dukanmu muna kama da tumakin da suka ɓace; kowannenmu ya kama hanyarsa." (Ishaya 53:6)

Ana iya taƙaita wannan ayar a cikin kalma ɗaya: tawaye. Wannan shi ne zunubin gama gari na dukan ‘yan adam. Annabin ya ci gaba da cewa, "Sai Ubangiji ya sa hukuncin laifin mu duka ya auko kansa [Yesu]" (aya ta 6). Kalmar laifi (a Ibraniyanci, avon) na nufin "tawaye," "hukuncin tawaye," da kuma "dukan munanan sakamakon tawaye." A kan gicciye, Yesu—wanda ya maye gurbinmu, Adamu na ƙarshe—ya zama ɗan tawaye da tawayen mu ya kuma jimre dukan munanan sakamakon tawayen.

Wannan ita ce ƙofar zuwa gidan wadatar Allah, idan za mu iya riƙe ta. Wannan ita ce musayar: Yesu ya ɗauki dukan hukuncin da ya cancanci tayarwar mu saboda dukan alherin da ya cancanta—saboda cikakkiyar biyayyarsa—da aka ba mu. Ko da ta wace fuska muka dubi wannan musayar, cikakkiya ce. An hukunta Yesu domin a gafarta mana. An yi masa rauni domin a warkar da mu. Ya ɗauki zunubanmu domin mu yi tarayya cikin adalcinsa. Ya mutu da mutuwar mu domin mu sami ransa. An mai da shi la'ana domin mu sami albarka. Ya jure da talaucinmu domin mu sami yalwar Sa. Ya ɗauki kunyarmu domin mu sami ɗaukakarsa. Ya jure ƙiyayyarmu domin mu sami amincewarsa.

Ka dubi hoton ɗan tawayen a kan gicciye a cikin tunanin ka ka kuma san cewa kai ne ɗan tawayen nan—hakika, kai ya kamata a rataye. Amma Yesu ya maye gurbinka. Ba tawayenka kawai ya ɗauka ba, har ma da dukan munanan sakamakonsa domin ka sami dukan albarku na cikakkiyar biyayyarsa. Wannan aikin alheri ne. Ba za ka iya samun sa ba, ba ka cancance shi ba, kuma ba na ka ba ne. Akwai hanya ɗaya kacal ta karɓar, kuma ita ce ta wurin bangaskiya. Ka gaskata kawai.

Na gode maka, Yesu, saboda aikinka a kan gicciye. Ina furta cewa Yesu ya mutu da mutuwa ta domin in sami ransa. Amin.

© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.

**Abincin Yini** ★

Kwafi: WD-B097-119-HAU

Sabuntawa ta karshe: 09 Sept 2026

Yanar Gizo: Derekprince.com/ha/resources




© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.